https://chat.whatsapp.com/FK9DApum8np3UZe5pQXxy3

*KISHIYAR KABILAH...*

PROLOQUE....

_BY SURAYYAHMS._

_®Any resembelence of story or lifestyle shud be considered as a coincedence._

Daga cikin Littafan dana rubuta:
#Arne
#samarin shaho
#sakamako
#ajalinso
#Ahumaggah
#tuntuben harshe
#kudi kumbar susa
#takaicin wasu
#shade of rufaida
#fitar rana
#lamarin gobe.

#Witching hour

wajajen karfe uku dedei na tsakar Dare wanda lokaci ne da turawa ke kiransa "witching hour" ko "spirituql awakening" inda ratar dake tsakanin spritual world wato Duniyar mutattu dana rayayyu bata da wani nisa, wnn lokci shine lokacin cin kasuwar ko wani irin maita da manyan kungiyoyin asiri, Da shawagin bakaken fatalwowi da kuma bakaken Aljanu da kuma dukkan wani irin launin supernatural spirits dake yawo cikin dare a fadin duniya.

Cikin wata jeji ne mai tsananin duhun gaske wanda ko hasken tafin hannun ka ba lallai ka iya gani ba.

Banda sautin kafafuwa  babu abunda yake motsi ajejin adede wann lokaci.

Wata kibabbiyar mata ce mai tudun duwaiwaka gata da tsayi da kuxari ta fito bujum daga cikin wani kurmin ciyawa mai tsananin duhu jikinta sanye da fareren kaya kal mai kama da likkafani.

Wani bijimin bakin akuya ne a hannunta tana kkrin janshi da karfi ayayin da bakinsa yake daure da wani irin jan tsumma da aka masa xane da farin chalk layi layi.

tun daga samanta har kasanta farine babu dison wani kala ajikinta face dan wani jan kyalle data daure tagaban goshinta da shi, kafafuwanta ta babu takalmi amma haka nan take tsagawa cikin duhun jejin da alaman tana cikin gaggawa ne domin ta samu isowa wani tsauni akan lokaci.

Daga bayanta wata matashiyace wancce baxata wuce yar shekaru 28 da haihuwa ba,daga ita sai ita , batasako takalmi ba bare kaya bare kuma dan kwali, saidan farin kyalle na farin xani dake bisa karjinta data dorashi da kyau, bayan babu wani abu a fuskarta face xanen jan fenti a saman goshinta itama.

kanta sunkuye a kasa sai sauri take ayayin da take bibiye da matar dake mata jagora cikin jejin acikin gaggawa..

Tafiyar da baifi na minti goma sukayi ba snn suka billa adede wajen wani katoton fili wanda yake nan tarwal cikinsa babu komi sai shinfidaddyar farin kasa mai kyalli.

Filin shikansa bayyana yy acikin tsakiyar dokar jejin adede wann lkcin domin kuwa koina ajejin wani irin baqin duhu ne amma wann filin shikadansa yana fidda wani irin farin haske mai shiga idanu.

xubewa ƙasa agaban filin sukayi dukansu subiyu ayayinda jikinsu ya hau rawa suna karkarwa kar kar kar kamar wani iskan sanyi nadaban ne yake ratsasu.

Dattijayar matar ce tayi sauri tafito da wani dan karamin kararrawa ta dinga kadawa tana wasu irin maganganu can sai ga wani jibgegen dutsi ya bayyana agaban su mai shape dinsa kaman kujerar sarauta golden colour yanamai fidda farin haske, haske mai tsananin kashe ido ne yay walkiya sann wata bokanya ta bayyana akan dutsen girif tana xaune itama jikinta sanye da fararen kaya. Atake suka xube kasa gabanta atare suna masu mata sujada tamkar itace ubangijin su..

"Almighty Goddess of fire And revenge".

Tsawon lokaci kansu na kasa suna gaishe ta tana kallon can sama sai can snn ta miƙa xara xaran yatsun hannayenta ta shiga shafa bayansu daya bayan daya da shi duk inda taja sai jini ya fito wanda take kaiwa kan harshenta tana lashewa da alaman ta amshe xiyararsu snn xata saurare su.

Hannu ta daga dan ta basu daman yin magana Nan da nan dattijiyar matan tafara mata magana cikin harshen yarensu ta yarbanci acikin wani irin salo na tsananin girmamawa da ladabtawa.

Muryanta na rawa ta xube kasa Tace _"Gbogbo orișa yinyin ti ina Ati iku_
Meaning All hail,goddes of fire and revenge, tace naxo neman wani taimakon gaggawa ne awajenki ubangijiya ta,kafadun yarta ta dafa tana layi ma Allansun kamr wance xatayi mata kuka snn tace"All mighty goddess of fire and revenge,tonite i offer my doter to the arrow of your fire and revenge..

Cikin datsar numfashinta  da muryanta dake fitowa acikin amo mai tsananin kuwwa da ban tsoro goddess din tace "My child, what do you want?

Matar Ta dada rusuna kai har kasa snn tace "i want Justice for my doter, goddesss..we demand justice.

Goddesss din tasu sai tay shiru batace komi ba,
Sai can sanda ta kalle akuyar da suka kawo snn tay mata alama akan taja shi tsakiyar filin sann ta yanka shi ta xuba jinin sa awajen..

Yartan kuma ta umarce ta akan data ja katoton round circles a filin snn ta xagaye su dashi snn ta kunna wuta a kan layin shima wutan ya xagaye su.

Wani bakin kwarya ne ya bayyana ta mika musu suka amsa, nan da nan dattijayar matar ta janyo baqin akuyan ixuwa tsakiyar filin ayayin da yarta ta xagaye su cikin katoton circle data xana shi da kasa snn ta cinna ma circles din wuta suka tsaya daga ciki.

Akuyar suka danne a tsakiya fuskar akuyan na kallon gabar kamr yadda goddess din ta umarce su,a dede inda jinin yankan xai xuba matashiyar ta aje bakin kwaryan jinin akuyan na xuba aciki, sauran da ya rage suka bari ya kwalala akasa acikin wajen

dattijayar matan ce ta yanka wuyar akuyan amma bata sake shi ba harsanda jinin nasa ya cika kwaryan dake hannun yarta sosai.

Bayan sun kammala hakan nan suka kawo jinin dake cikin kwaryan har ixuwa gaban goddess dinsu suka mika mata cike da ladabi da biyayya, amsa tayi ta miƙa kwaryan jinin can sama, wani haske mai yawa yabi ta kai snn ta saukar Da shi ta hura iskan bakinta akai wani farin haske ya fito daga bakinta ya shiga cikin ruwan jinin gabaki dayansa snn ta saukar ta basu dukan su sukayi kurbi daya, bayan nqn tawatsa ma matashiyar budurwn sauran jinin ajiki Wanda atake ta fadi kasa ta suma sabida spritual electric shock din daya kwasheta.

Bayan hakan ya faru ta juyo ahankli ta dube dattijiyar matar dake tsaye kanta a kasa tanamai jiran hukunci dq harshen yaren su tay mata magana snn tace mata menene sunan yaron..

Kan dattijar matar na kallon can kasa tace sunan shi "AHMED DAMILARE BELLO son of BELLO Ayodeji JIMADA.

Goddess ta jinjina kai tace and the girl in question?

Tace "Efik girl, born by an igbo woman.

Goddess ta kalli can sama snn tayi wasu maganganu da yare sosai tanayi tanamai bushewa da dariya mai kara.

Can ta tsaya cak da dariyar snn ta juyo tana kallon matar ido da ido

tace "you can go now my child. ur work of revenge is done (ki je, aikin ki ya kammala)..

Ni Allahn ki inamai baki tabbacin cewa Ahmed, son of bello jimada and his wife doter of effiong will never bear a child
..NEVER.

Acikin harshen yaren su tace"rashin haihuwar nan shine xai xamo silar rashin farincikin auren su ta har Abada. Snn yarki ce xata kasance musu kashin kifi a wuyarsu dan haka na baki ixinin kaita cikinsu.

Goddess Tana kammala fadar hakan ta bushe da wata iriyar dariya ayayin da dattijar matar ta xube kasa tanamai mata godiya sosai

...sai can ta bace musu bat tare Da filin duka da kuma wutar da komi ma sai wajen ya dawo kamar ba wajen ba,dan ganin kansu kawai sukayi agindin wani katoton bishiyar mangwaro mqi tsinannen duhu suna tsaye, wani katoton duji mai manyan idanu na gabansu ya xuba musu ido yanata kallonsu.

jan yarta dake layi tayi suka fice ajejin acikin gaggawa dan wajene mai hatsarin gaske. After like 20min suna gudu suka kai bakin hanya suka shiga cikin motarsu acikin sauri nan ne kowacce acikinsu tamaida abayarta ajikinta snn suka kama hanyar xuwa gida.

Koda suka isa gidan nasu dattijiyar matarce ce ta rirriko yarta dake layi ixuwa dakinta cikin kulawa sosai ta kwantar da ita tanamai rarrashinta dan ta samu tayi bacci..

Sai kuka yarinyar take dan Da sunan Ahmed din abakinta baccin ya kwasheta.

dattijyr matar ta jima axaune tanamai kallon yarta dats looking helpless and heart broken ,atsaye ta mike tanamai sauke huci mai xafi Aranta tanamai cewa Familyn Bello jimada saiku shirya cos i fatihat adetunji balogun am coming for u......
SHARE PLEASE

FOLLOW WATTPAD @ SURAYYAHMS

CONTACT 08060712446
CHATS ONLY NO CALLS[5/28, 9:20 AM] SURAYYAHMS: *KISHIYAR ƘABILAH...*

_BY SURAYYAHMS._
Wattpad@Surayyahms.

_®Any resembelence of story or lifestyle shud be considered as a coincedence._

Bi-ismillah..

Episode1️⃣

A hankali yake kai desert din dake gabansa ixuwa bakinsa kansa a sunkuye yana dan murmushin nan nasa mai kyau da ya kai ga har ana iya ganin lotsawar dimples dinsa.

Acikin sigar nitsuwa da kamala sosai yake xaune jikinshi sanye da wata petite cambridge grey colour zegner french suit dinsa datamai kyau ajikin shi bana wasa ba.

Sassanyar muryan mahaifyarsa ne yake ratsa shi,ahnkli ya dan girgixa kai snn ya dago lumsashun idanunwansa yana kallon dattijiyar matar dake Zaune akan kujerar dake kallon nasa fuskarta a daure takafa masa ido tana kallonsa, "murmushi yakuma yi mai sauti xai yi magana ta rigasayi a fusace tace "ohhhh,ni ce ma na xama abun dariyarka yau ko Ahmad? Maganan yarinyar nan kafayat fa nake maka but ure busy smilling at me kamar wani abun arxiki nace ka aikata mata..arent u ashame? Yadda ta karashe a fusace yasa shi kara sakin murmushi wanda ya dada tunxirata,
muryanta cike da fusata tace "ohhhhhh wato ga mahaukaciya nan na maka ihu ko,Ahmed are u out of ur mind?..

Babu shiri ya dan marairaice fuska snn ya ajiye fork din hannun sa da murynsa mai taushi da dadi kasa kasa yace pls calm down, i am really sorry maa, wallh ba haka bane Mamee,ni nama isa in maidaki mahaukaciya ne? ai naji me kikace akanta, toh ni wallh bansan ranta ya baci ba ma saida kika fada ynx,toh wai meye nata na yin fushi ne dan ban tsaya a wajen birthday partyn ta ba sai kace wani ni saurayinta ne? Wani ruwan Takaici ne taji ya shake mata makwogoro daya furta hakan.

tsimewa tay bata ko kulashi ba dan tasan ranta ne kawai xai kara baci inta tsaya yin masa wani bayani, baki bude take kallonsa acikin yanayin mmkin halin basarwa irin nasa yo ace duk wani

walakanci da cin fuskan dayay ma yarinyar nan agidan nan shibaima san yana yi ba..

Kyabe bakinta tayi tanamai karkada kafafunta aranta tana jin tsananin takaicinshi ayayinda take tuno da irin baqar wahalar da kafayat din tasha agidan nasu kwana biun nan, wani irin sihirtaccyar ajiyar xuciya mai nauyi ta sauƙe cos Kafayat whud have been the perfect doter inlaw and a responsible wife for her son Ahmad domin yarinyar nan itace ta san shi tun suna yan kanana tun basu san kansu ba suke abota.

Gashi tun xuwanta Nysc take xama dasu agidan dan sabida tana kulawa da su na musmn sabida son Ahmed din datakeyi aranta duba da shine first love dinta, hatta mahaifin sa ya bala'in amincewa da kwaxo da kuma halayyar kirki irin na kafaya,gata nan masha Allah black beauty omo yoruba, gaba da baya full option,gata da tsafta, ga son shara, ga iya wanki da guga, ga iya wanke wanke,uwa uba ga iya girki,ga kuma ladabi da biyayya,duk tayi musu luguden hidima agidan sabida shi amma waishi baima gani ba.

Acikin sassauto da muryansa kasa kasa sigar lallami yana kallon yanayinta yace iyami",my mamee, harararsa tayi tun bai fara mata dadin bakin ba, yace "toh kiyi hakuri mana mama naa inadai kafayat buraimo ne?i promise i will apologise for ur sake! kikace wai dan naki attending birthday din da kuka hada ne yasa tayi fushi ta bar gidan nan ko? Lumshe ido tay dan harynxu mamki yake bata ganin cewa baima san lefin daya aikata ba, Girarsa ya dage sama ahankli, da har dai xaice "She is soo silly" sai kuma ya kumshe sauran maganan abakinsa yy shiru,dauke kan datayi yasa ya dan shafa kansa da yanayin damuwa a muryansa yace "mamee pls now, kidena fushin nan mana nide nasan damuwarki bai wuce kice xancen relashp dina da kafayat ba,i told u i need time..kuma aikinsan komai fa lkci ne, AUREN nan xanyishi in lkci na yayi,kawai su Dad sun kasa gane hkn ne kema kika bi bayan su,sun ki fahimtar abinda nake nufi batun auren nan,i swear im still searching for a good nd decent wife just for u,kuma nasan idan lkci na yy na aure xan kawo muku matar Aurena ko ba kafayat ba,am just bored of all dis match making da kuke min. Kubari mana uhmm iyami?..

Ta cigaba da kallonsa rai bace batace mai uffan ba,shafa kansa ya kuma yi har lkcn fuskar sa na dauke da damuwar yanayinta dan sosai ya tsani yanaganin bacin ranta,saidai shikansa baisan mesa suka saka kafayat aransu hr haka ba, sallamar da aka yi ne yasa duka suka maida hankalin su ixuwa ga bakin kofar tare da amsa sallamar baki daya.

Mikewa tayi ganin yan uwan mijinta ne suka shigo su subiyu, Anty temi (ramotou) da anty (moslimat) Mojushola,da wata kyakyayar budurwa mai suna maryam wacce kallo daya kamata ya ishi kasan bahaushiya ce,da fara'arta ta tarbesu tana masu sannu da zuwa basu wani tanka ta sosai ba suka karaso cikin falon aka shiga gaggaisawa sama sama dan duk hnklinsu da nitsuwarsu nakan dan saurayin ne.

A cikin nitsuwa ya rusuna ya gaishe su snn ya mike tsaye yanamai kallon mahaifyar tasa, adan gaggauce yace "mamee ni xan wuce sai na dawo ko xuwa gobe"..kafin ta amsashi har Anty Temin tay sauri ta amshe xancen cikin sautin babban muryanta na giant woman, fuskan ta babu

alaman fara'a tace "oshey Damilare, wat do u mean by dat statement? _Ahhh dami, iwọ ko si oju iberu ti o ni ibanujẹ?_ (ahhh dami,u no dey fear face?)..Daga xuwan mu ne sai kace gobene xaka dawo? but Dats not fair oo,ta kalle babban dadan su da batace uffan ba cikin bambami ta karashe xancen fuskarta a daure "Ahhh see Shildren of now adays,kadai dawo xuwa anjima kar kakai daddare dan bamu gama magana dakei ba, tana maganan tana kallon  cikin kwayar idanunsa suna hade ido sai ta kalle budurwan data sunkuyar dakai kasa da alaman ta fahimtar dashi abunda suke nufi, ahnkli yyi murmushi yace its okay "toh in' sha Allah xan dawo anty rahama.

Shiru tayi batace mai uffan ba sabida she love them to be adressing each oda da sunayen yaren su amma sam shi bayaji, shiyasa ma ita sam bata kiransa da  Ahmad aganinta sunan hausawa ne irin na maman sa, sudei a fannin uba saidai sucemai "DAMILARE " ko "DAMI" KO "LANRE" sabida sunan nasa inkiyar sunan baban mamansu ne so they respect dat name alot.

duk maganan nan da ake Anty mojushola batace musu uffan ba banda cika iska da hura hanci da yatsine datake bin su dashi, dan itadin ta manyanta sosai dan itace first female child da mahaifinsa yake bi,sai uncle dinsa bakare,anty temi (ramotou) kuma itace autarsu.

Bayan sunyi hakan sai yyi musu sallama ya fice daga falon yana kallon agogon hannunsa daga nan yanajin anties dinsan sunakan watsa habaici wa mahaifiyarsa na cewa tunda yaki auren mace daga kabilarsu aiga nan bahaushiya sun kawo masa daga nata irin kabilar, sam dangin mahaifinsa basa da sauki,they just love to be in control of evrthing. A farko ma sunedai suka soma cusawa kafayat ra'ayin xama agidan iyayensa dan tana musu bauta,so during her nysc session sai ta xo just to get his attention ayi aure, dukkan dangin ubanshi suna matukar son ace kafayat ce ta auri Ahmed just for the simple fact that itama kabilar su ce na yoruba.

gun motarsa ya nufa da sauri yana tafe yanamai kallon agogon hannunsa acikin gaggawa ya buɗe ya shiga ciki ya kunnata da sauri yabar harabar gidan nasu.

Ahankli yake tukin aransa yanata tunanin yadda xai kawo karshen wann matsalar data kunno masa kai acikin familyn sa musammn na yadda kowa yake son yaga lallai ya aurar dashi acikin gaggawa..

After some few hrs...

_National communicable disease control Theathre hall maitama Abuja._
_5.56PM_

Manyan likitoci da public health professors ma'abota ilimi da wayewa da kuma kwarewa a bangaren yaƙi da yaɗuwar cututtuka ke shige da fice a babban hall din NCDC dake garin Abuja

kowa da alaman fara'a akan fuskan sa.

Lectures din da suka yi yau was very interesting Dan Sai yanzu duka suka fahimci abinda minister of health na kasa yake nufi a lokacin da yake
ce musu the youngest professor dinsu AHMED BELLO JIMADA is the best and leading young epidemiologist da sukay employing acikin CCD project dinsu na wnn shekarar sabida yanada gwaxo sosai,snn yana bin komin sa ne a dalla-dalla cikin nuna ilimi da kamiya. And He makes sure He carries everybody along acikin kwarewarsa. Snn Yana making good references da abubuwan da yaje ya koyosu a kasashen waje yanamai kara budasu tareda yin gamsashen bayani akansu using simple terms wanda ko the most dummiest and stupidest person zai fahimce shi.

Yau yay musu electronic lectures ne akan manyan pandemic and prevalant diseases dake addaban iyakar boundaries na tsakanin kasa da kasa kamar su COVID19,i:e corona virus, Acquired immuno-deficiency syndrome(AIDS) da severe acute respiratory syndrome (SARS)da wasu ire iren viral flus.

Anan kowa ya kara fahimtar cewa shi mutum ne mai tsantsar nutsuwa da ilimi, komai nasa a hankali yake yinsa. He is very gentle bashi da hayaniya sam saidai daga ganinsa za ka iyasanin cewa yana mugun ji dakansa sabida wani irin tsantsar self assurance da kuma zazzafan self confidence dayake nunawa ayanayin sa musammn in yana fidda bayanansa acikin kwarewa da ilimi daya gama ratsashi.

Wajajen karfe biyar ya wuce suka kammala lectures din ya fito cikin takun nitsuwa jikinshi sanye da hadadden petite cambridge grey suit dinsa dayake wani irin fallasa tsantsar burgewan dake tafe da karancin shekarunsa dan matsakaicin 32-33yrs da haihuwa as one of the current youngest leading professors and doctor of epidermiological science a Abuja.

Prof.Dr Ahmed bello jimada kyakkwa fari ne amma ba fari can ba dan za'a iya kasa shi acikin light skin yoruba demons mai yanayin tsiririn hanci da fuskar uwarsa ta asalin fulanin garin illori..

Saidai kuma da akwai wnn kamannin da kuma zubi na Jinin mahaifinsa na cikakken bayarben oyo state msmn ayanayin ginanne kuma tsayayyen siffar jikinsa da kuma yanayinsa mai tsananin burgewa,yana da cikakken saje da dan matsakaicin gashin gemu da kuma fasalin kamala ta kyawawan mazajen arewa daya debo acikin jinin xuriar mahaifyarsa.

A matsayinsa na matashi mai ji da ilimin zamani da kuma wayewa da daukaka yasaka yake da karancin lokacin yin sabbin abokai bare kuma ajega yan mata,daga scndry schl har izuwa jami'an dayay baida sabbin abokai duk abokansa na yanzu tun na childhood dinsa ne.

iyakan aikinsa da karatunsa sune kawai agabansa cos he alwys believe serious girl friends and new friends to be a distraction to his career and success, shiyasa ko wani soyayyar arziki bai

taɓa tsayawa wajen yi arayuwarsa ba saidai yayi soyyaya ta sharholiya na lkci kalilan.

In his life dan yay keeping companyn mace na kwana biyu ko yay tarayyar sati daya ba wani abu bane sanin cewa lokcin aikin sa nayi to shikenan soyayyar ya kare,shiyasa shi bai taɓa cewa yana son kowacce mace dagaske ba,saidai duk wacce taƙuso masa kai ta kawo kanta wajen shi zai iya bata lkcin shi na kwana biyu ko sati guda da ita daga nan in aikinsa ya tashi bazata kara ganin idonsa ba.

Mata dayawa har sunyi sun gaji sun hkura sun dena sakashi aran su sanin cewa inya gama da mace xai iyayin ma kamar bai taɓa ganinta arayuwrsa ba, halin sa yasaka mata dayawa ke muradinsa a matsayin miji cos he is really hard to get type,yana da high taste wajen xabar macen da xaiyi tarayya da ita,shi irin kalar maza ne da mata ke mutuwar son kasancewa da su sabida yana da sakkaken hannu kudinshi bai dame sa ba, saidai shi namijine da bai da saukin kai,ba asaka shi ba kuma hana shi,he alwys need to be pleased gashi da tsinannen shiga rai da iya nuna ko in kula da komi musmmn ma in amfaninsa ya kare agaresa.

mata dayawa daga  nigeria har waje sunsha sako burin su akansa kodama zai tsaya ayi wata magana ta soyayya da aure amma haryau baida wann ranar bare kuma lokci,wasu sunyi sunyi tun yana 20s har sun gaji till he is 33yrs old now kuma babu abunda yanema ya rasa arayuwar sa, ilimi, kudi, kyau, gata, snn shine namiji daya talli kwal awajen mahaifyar sa mai suna hajiya khadijatu muhammad gidado wanda takasance cikakakkiyr bafulatana ce a garin kwara,jihar illori.

Ahmed yay karantunsa ne adan kankanin shakeru sabida irin kyakkyawan kulawar dayasamu arayuwarsa yayunsa uku da suke uba daya uwa daban daban duk sun girme shi nesa ba kusa ba kuma kowannen su yana kulawa dashi sosai.

mahaifinsa Alhaji Bello Ayodeji jimada,bayarbe ne daga garin oyo,jihar ibadan, shi kabilar yoruba ne da sukayi xaman cirani da lumana tare da fulanin garin illorin,a sanadiyar rasuwar matarsa na fari wato alhaja simiat laide ne ya auro matarsa na biyun bafulatana wato hajiya khadijatu muhammad gidado wanda itace ta rike masa sauran yayansa.

Babban dansa shine Kazeem wanda ake cewa Aremu (Qasimou) sai mabiyinsa hamzat Dimeji (hamusé) da kuma ta mace wato Zainab moturayo (senap) kafin nan Ahmed(Damilare)

Ahmed shine dan Autan gidan nasu,ya kammala first degree dinsa ne a can obafemi awolowo university ta ibadan oyo state garin mahaifinsa while he is 21yrs,yay masters dinsa a kasar waje acan United kingdom for 12month afannin CCD(control of communicable disease)
Sauran kuma ya karasa a university of manchester wanda sabida gwaxonsa ne yasa he became the youngest professor of comuncble disease at age of 31, bayan ya kammala karatunsa 2yrs ago ne yafarajin kamar is high time yafara enjoying life dinsa.

saidai wani hanxari ba gudu ba, his family only desperately wanted him to get married akan

lokci sabida Xpectations dinsu kenan akan duk wanda ya kammala karatun sa ya kuma samu dukan wani achievement dinsa na rayuwa sabida su kare mutuncin yayansu dana xuriarsu daga haifo yayan shegu awaje.

saidai shi har yanzu shi bai da wata tsayayyar budurwa bare ajega matar aure dan baisan yama za'ayi ya fara soyayya ba bare aure snn har acikin xuciyrsa in akwai abunda ya rantse baxai amince ya yarje akansa ba shine auren hadi..

SHIN KO YA XA'AYI AHMED YA KAWO MUSU MATAR AURE?

#SURAYYAHMS grp
08060712446 chat only no calls.
[5/28, 9:20 AM] SURAYYAHMS: *KISHIYAR ƘABILAH...*

_BY SURAYYAHMS._

_®Any resembelence of story or lifestyle shud be considered as a coincedence._

Daga cikin Littafan dana rubuta:
#Arne
#samarin shaho
#sakamako
#ajalinso
#Ahumaggah
#tuntuben harshe
#kudi kumbar susa
#takaicin wasu
#shade of rufaida
#fitar rana
#lamarin gobe.

Episode2️⃣

Wajajen Shida da rabi saura na yamma Dr Ahmed bello jimada yabar headqtr nasu na nigerian disease control ya kama hanyar gidansu dake cikin jerin layin masu kudin anguwar Katampe extenstion dake abuja.

Ahnkli yake tuki yana jan tsaki har ya iso kofar gidan nasu yay horn a bakin gate mai gadinsu ne

yazo agurguje ya buɗemai snn ya shigo ciki batare da ya kula shi ba.

Babban compound ne sosai dake dauke da shuke shuke da bishiyoyi masu daukar hankali, kai kana ganin tsakar gidan kasan kwanciyar hankli da wadata ta zauna.

mahaifinsa Alhaj Bello Ayodeji jimada also knwns as professor Bello jimada(prof BJ) babban manomin shinkafa ne kuma kwararren tsohon professor ne a fannin psychology, wanda ilimi da wayewa yagama ratsashi.

makeken tsakar gidan nasu na dauke da sassa har biyu masu design iri daya,snn ko wani sashe akwai tazara mai dan tsayi tsakaninsa da wani sashen, sashin farko wanda shi zaka ci karo dashi bayan shigowar ka cikin gidan shine mai bungalow dinsa yana da girma sosai don sashin ya fi dayan sashin girma.

Sashen da baida girman ya wuce kai tsaye snn ya haura sama yawuce side dinsa tun anan falonsa ya fara rage kayan dake jikinsa yana yardawa nan kasa while walking like a fierce model cos he have the perfect manly fitted shape and muscular figure.

Ann Cikin part din dake cikin na mahaifiyarsa nasa sashen yake dan kuwa na musamman aka sake gyara yanayin building din tun alokacin da aka haifesa,shiyasa he have his very own parlour da bed room da closet inda ke lode da kayan sawa kala kala masu tsada da kyau. Ya xabi xama a sashen mahaifyrsa ne sabida yafi sakewa sosai da ita. In ka shiga Bangarensa zaka san indeed shi dan gatane awajen mahaifiyarsan..

Bangarensa is well organised kamshi wajen yake kowani lokci sabida kulawa masa dashi datakeyi sosai,dan madaidaicin falonsa mai kyau na dauke da set of expensive and luxury sofas sai madaidacin tv plasma babu wani tarkace ,yana kaiwa tskiyar dakin nasa ya jefar da takalmansa snn ya wuce wajen wanka direct,.

Anan ma Sai da ya kusa hour guda acikin bathroom babu abinda yake sai shafawa kansa ruwa da sabulu ahankali kaman akansa aka fara sauke kalman lalaci da gajiya,sai can daga karshe snn ya fito daure da towel yana goge kansa da wani dan karami,soft palmers cocoa butter oil ya hau shafawa a jikinsa daga sama har zuwa kasa, sai da ya gama yadauko doguwar jallabia kalar toka ya saka ta with small tiny shorts daga ciki. Ya fetsa turare mai sanyi, da Har ya fito zashi masallaci sai ya tuno da mahaifinsa, sai kuma ya fasa ya kulle side din nasa da keys, Sallahn magrib da isha'i yay,snn ya nemi waje ya xauna akan sofa yay zugum harna dan wani lkci.

jin yunwa na neman damunsa yasa ya bude fridge dinsa ransa a harɗe da baiga wani abun kirki anan ba..

Da har xai rufe sai yaga wani shiny leather acan gefe, budewa yy batare da ya dago ba, Birthday cake din da chilhood friend dinsa kafayat buraimo ta aje masa ya gani a aje,

gajiyayyen tsaki ya saki aransa yana jinjinawa kalar xubda aji irin nata,wasu dai haka Allah yayisu basu da aji sam sam, kyabe bakinsa yy tuna yadda yake mugun ja mata aji, birthday din da tayi tayi ya saka kanshi acikin hidiman amma yaki to me na aje mai cake duk da uban walakncin daya mata? Girarsa na sama a adage yasaka hannu ya dauki cake din yafaraci kamar dole, yana taunawa yana tunawa da wagagan lips dinta yana jan tsaki dan aganinsa halittar labbarta daya danyi kato shine kawai ya ɓata ta, but after that she is clean gata da diri mai daukar hankli. Sede shi sam baisan mace mai katoton baki da girman nono. And kafayat can talk for africa kai kamar ma dan shegen son gulma da shishiginta yasa Allah ya bata kyautar katoton baki. Haka nan dai ya rinka debe mata albarka aransa yanayi yanacin cake din kamr ansaka shi ci dole.

Sai can ya koma kwanta ahankli ya fara resting mind dinshi for a while acikin yanayin lumshe ido iya abubuwan da iyayensa ke yawan gaya masa na batun kawo matar aure sune suka fara dawowa masa akansa daya bayan daya.

Tare da sakin wata shakurarren tsaki yay kasalallen juyi tare da pillown dake manne akan kirjinsa jin kamr cake din ne ya tokarasa akirji.

Shi Duk yan matan dake bibiyarsa haryau bai ga wacce ta masa daya aura ba,tashi zaune yy cikin damuwa, but how comes he does not have feelings for any girl even kafayat dat was his best friend tun na yaranta data san abubuwa dayawa game da rayuwarsa amma bai taɓajin tai masa aransa ba harynxu.

Dada taƙure kanshi yay cikin zurfin tunani tare da tunowa da maganan daya daga cikin babban yayansu wato brother dimeji a.k.a hamzat bello jimada da yake cemai hala shine dai bai nitsu ya gano tashar wacce zuciyarsa take so din ba.

But Ders are so many girls going after him taya ne ma zai gane wacece aciki yake so mtschew! a iya tunanin su ma kawai wani ciwon kai da wahala yake kawo masa,
Ynx bbn matsalar sa shine ya rasa gane wacce ce special girl din acikin babes din daya taba sani arywrsa, ance dai ur special girl itace wacce tafi fadowa cikin ranka amma sai yay kwana fiye da talatin bai tuna kowace ya mace aransa ba,gara gara ma his childhood friend din kafayat obviously sabida tana yawan kiransa a waya, alwys acting like his wife, bayan ita then there is this innocent yarinyar data dan kula dashi sosai wani lokci dayaje research dinsa a garin cross river calabar wanda yasan dai sai yana cikin wani damuwa ne yake iya tunowa da ita cos she helped me more than anyoda girl can arayuwarsa.

Kuma harga Allah sukadai ne matan dayasan yake iya tunawa dasu aransa involuntary sabida koba komi yana dan iya sake jikinshi dasu sosai, but in his heart kafayat is just a friend and Adiaha was just a helper.

Altho ADIAHA, was just a coincedental friend baxai iya cewa budurwansa bace..

Wanda yasan hala da baije aikin research agarin su ba dabazai ma santa ba, but despite being a typical IGBO/EFIK girl itace dai ta taimakesa sosai,tana da sakin fuska tayi masa hidiman abinci,ga kulawa na musmmn data bashi dayaje aiki a garin calabar during his scientific research programe na lassa fever.

Life was indeed calm with her dan yarinyar sam bata da hayaniya.

Saidai ayanzu baisan ko inya koma wajen zaije ma ya sameta ba dan tun daya kammala damuwar sa a calabar yabar wajen baisake nemanta koda a waya ba. Yasan hakan dayay xai iya bata mata rayuwarta, He is sure hala ynxu har tay fushi ta mance da shi kamar yadda sauran yan matan dayake dumping dinsu a rana tsaka suke yi.

Wani gullutun Tsaki ya ja tare da sauke pillon daya rungumar akirjinshi yanamai jin haushi kansa a karo na farko dan baisan meyasa ya kasa neman yarinyar kodam yy mata godiya ba.She was nothing but good to him, innocent and care free, sau tarin yawa tayi ta kkri wajen nuna mai irin kaunarsa datake mutuwar yi aranta saidai bai taba nunawa cewa yasan da cewa tanayi ba cos dats was his habits alwys. Yana son yaga mace tana son shi yana nunawa kamr baisan tanayi ba. He love to ignore ppls feelings cos he is self obsessed kuma yana mugun ji dakansa bana wasa ba.

Ko aynxu Ya tabbata dan acikin matsi xcyrsa take da ko kadan baxai tuno da ita ba,Sassanya kuma nitsutsyar murmushin ta ya soma tunawa yanamai jin sauyin yanayi mai tafe da bugun zuciya atattare dashi. yasan dai yay kuskuren rashin yi ma zuciyarta adalci msmn daya guje mata batare da cemata komi ba,she is faultless saidai shi ba mutum bane mai son tunowa da kuskurensa dan haka sauri yay wajen kawar da wann feeling din aransa na jin cewa yay mata rashin adalci dan kar ya karaya sosai,Ransa a dan hargitse ya sauƙo kasa daga kan gadon kamr ana ingiza shi, yarasa meke masa dadi, ruwan sanyi yaso daukawa a fridge dinsa sai yaga babu mai sanyi sosai dan haka acan gefen gadonsa ya tsuguna tare da buɗe bedside drawer nashi da key,ya ciro wata kwali aciki ya fidda wata kwalban wine mai tsada dayazo da ita daga UK.

Ya dade da dena shan giya amma ji yake yana bukatar sha sabida  yadan ciremai tunanin komi musmmn ma na auren nan dayake dagula mai kwakwalwa, nan ya buɗe kwalban yafara sha ahankli after a while ya yarda kwalban akasa ya kwanta batare da yin tunanin komi ba daga nan sai bacci.

Washe gari da safe
Farakal din Agogon dake manne jikin bango ne yayi ticking dot 6:30am dai dai na safiyar ranar friday tare da yin sautin alarm mai karar water ascent wanda tuni ya gauraye wajen da wani irin kara mai cikka kunne,

tashi yayi firgit tare da miƙewa daga kan lallausan katafaren gadon da yake kwance akai,yana mai dafe kansa datake mai nauyi.

Dagowa yayi sann ya juya ya kalli agogon da ya farkar dashi daga bacci yaga har 6:35am tayi, da dan hanzari ya diro kasa daga nan baijira ba ya fada toilet din dake cikin dakin shi cikin hanzari ya saka toothpaste ajikin brush dinsa wanda yake fari kal da sauri da sauri yayi brushing teeth dinsa ya kunna warm shower yay wanka sannan ya fito daga toilet din daure da hadadden white body towel da kuma wani dan karamin towel din a hannunshi yana famar goge fuskarshi da ita har ya karaso gaban wani babban mirror da mutum kan iya kallon kanshi tun daga kai har kafa yana mai kare ma hadadden dirinsa takaitacen kallo tare da sakin nannauyr ajiyan zuciya, sake tunowa da lamarin Adiaha daya karayi aransa yasashi lumshe idanunsa tare da buɗewa ahankli cikin rasa dalilin dayasa ya fara sakata aranshi.

Dagata cikin mirror ya hango empty wine bottle dinsa akasa dayasha jiya yaja tsaki bai kara kallon wajen ba yafara goge kanshi cikin saiɓi.
Aransa yana mita yana cewa Inba irin wann damuwar auren ba maixai saka shi yasha giya dan ya samu nitsuwa?

yana cikin karasa goge kanshin kenan zai shafa mai yaji karar wayarshi na ringing,Dan daga girarsa sama yy da har yayi kaman bazai dauka ba sai kuma ya juya ya karasa inda wayar take yana ganin mai kiran da sauri yayi maza ya dauki kirar tare da neman wajen zama cikin risina kai mai nuna alamar tsantsar girmamawa tamkar mai Kiran na gabanshi zama yayi kamin ya kara wayar a kunnanshi tare da cewa

"mamy na kin tashi lpya?

Daga daya bangaren aka amsa da murya kasa kasa da cewa lpya lau Alhamdulillah ,sannan ta sake ce mishi Ahamad harka shirya ka fita ne?

Fuska ba yabo ba fallasa yace à ah mamy Amma saura kadan yanzu zan shirya in fito ina dan sauri ne yaudin..

Ajiyar zuciya ta sauke snn tace ok toh kadai sauko din, na shirya maka breakfast inajiranka akasa inason magana dakai. Take yaji walwalar fuskarsa ta dauke tuna cewa basuda wani maganan da suke masa a kullu yaumin face na AURE ita da mahaifinsa, da can dai yadauka wa yan mata kawai ake irin wnn takuwarar akan suyi aure subar gidan iyayen su amma sai gashi shima baida katabus agidansu sabida duk sauran yayunshi suna da aurensu shine kawai ya rage baiyi ba, adan gaggauce yace "toh" Yana fadan Hakan ya katse wayarsa batare daya jira Wani furucinta ba, da alamar ranshi bai wani so amsawar dayay ba.

Tsaye ya mike cikin sauke huci tare da yin wani ball da empty wine bottle din yanamai turasa cikin karkashin gadonsa.

Closet din kayanshi ya bude sannan ya dauko wani true blue men suit mai laushi da tsada ya saka ajikinshi,ya bude wata madaidaicyr transparent safe ya dauko nordstrom neck tie dinshi marching colour mai azaban kyau na kamfanin steve sannan ya sanya ya masa das,agogon shi na rolex submariner ya makala a hannunshi na dama sannan ya dauki
Turaren paco rabane  dake gaban mirror dinshin yafesa a jikinshi Duk Inda ya juya kansa qamshin ne ke binshi.

gaban wata small coffee table ya Mika hannu ya dauki car key din motar sa dake ajiye akai da kuma wayarsa daya jefata acikin aljihun sa sannan ya jawo takalmin shi baqin cover shoes mai sheqi yasaka a kafarsa snn ya fito daga dakin yana saukowa yana dan kallon agogon hannun shi yaga wai har bakwai da rabi tayi.

Saukowa yake daga kan benen cikin kwanciyar hankali da natsuwa har ya karasa sauka ya isa katafaren parlourn su.

karasowa yayi cikin parlourn ya isa wajen mahaifyrsan dake tana da dan haske tasanya wani babban atamfa purple colour an mata dinkina alfarma sanye take da farin gilashi à idonta Gabanta kuma 10 inches dinning table ne dauke da hadadden royal flask din tea tazuba Kadan a dan karamin transparent kofi na shayi tana zuƙa ahankli, Nan ya karasa gaban ta tare da zama dab yana kalle kalle can snn yace mamy yana ganki ke kadai anan, DAD fa, kodai bai farka bane?

Sauke cup tay agabansa ayayin da tadaga idanun ta sama tadan kallesa kadan tace badai bakaje sallahn asubah yau ba?

Fuska ba yabo ba fallasa yace na makara, tace hmmm shiyasa, Baban ka tun a lokcin ya fita, Jiya ya tura da saƙo wajen ka an sanar maka?

Dauke kanshi yy kmr Bai amsa ta ba ya girgiza kai. Bata kulashi ba tace malam liman yace min wai jiya ka dawo da wuri amma kuma ka rufe kofa kuma wayoyin ka ma duk a kashe. a kasale cikin rashin son jin maganan Yace mamy nagaji ne shiyasa nay bacci da wuri. Cup din data aje mishi ya dauke ya kai baki badon yay niyya ba
Ya kurbi kadan snn ya sace kallonta yace Mamy Pls lest have our breakfast now in mungama mayi maganan later, batace mai uffan ba ta zauna tafara serving dinsa beans cake da wainar panke, har ya deba yafara kaiwa bakinsa kenan yana taunawa sai ya dago kansa sama caraf idanunsa suka fada kanta ganin yadda ta rabza wani irin tagumi tabi ta zubamai ido tanata kallon sa cikin yanayin matsanancin damuwa da zurfin tunani.
#surayyahms
08060712446
Follow wattpad @surayyahms.

[5/28, 9:20 AM] SURAYYAHMS: KISHIYAR KAƂILA....3

Sihirtaccyr Ajiyar xuciya mai nauyi ya sauke snn ya dauke kansa akanta jin har tafara fidda masa abubuwan dake wakana daga cikin zuciyarta na irin maganganunsa da sukayi jiya tare da su anty mojushola da dayan antynsa ramatou.

Cikin gyara zaman farin gilashin dake sakale a  idanunta ta karashe bambaminta da cewa Ahmed ai kasani sarai cewa Kafayat itace xabin su kuma sunsakata aransu sosai amma haka kaki kula yarinyar nan sam ka watsa ma kowa kasa a ido,let me inform u dat ur aunt ramatou is soo pained dataji wai baku fahimce juna da kafayat ba,and ur aunt moju is even worst, cos she is not even talking to ur father,ko gaisuwar sa ynxu bata son amsawa,ai kasanta yar debar xafine.
  she is just blaming me up and down dan haryau gani take kmr nice nake controling din rayuwarka kaida ubanka, tace komi dake faruwa ynxu lefina na ne, waini na mallake ubanka na rabasu da shi sai abunda nace masa kawai yakeyi.

"Ni har na rasa mema xance musu,iya Rashin dawowarka gidan nan jiya bakaramin jamin cin fuska yyi ba,Ahmed ure just too stubborn, kai dakanka u knw how ur anties behave with me, amma kodan ni baxaka iya behaving kanka na Ikci guda ba?sai kasa surika maida duk wani abunda ka aikata akaina dan awajen su nice nake daure maka gindi a gidan nan?gaskiya baxata saɓu ba, Enough is enough Ahmed! Wallh ka shiga hanklinka dan ni nagaji da ku baki daynku baku kuka kawoni duniya ba.
  kadena kuma jin kanka kamr kafi karfina cos ure still my child,in har na isa dakai ina son ka tabbatar min da haka ta hanyar yin abunda nake so kawai, Ahmed for the last time yau ina gaya maka ka kawo mana matar aure, bana sonjin wani dogon bayani daga gareka anymore.

Dan ina daga maka kafa dole ne abun naka yafara wuce misali,km bawai dan duk wani abun dakake aikatawa da rayuwanka awaje ban sani bane wallh nasani sarai cewa kana tarayya da yan mata,i dont care how u wil do it..nide kaje ka kawo min mata acikin su kowace ce cos i am tired of cin fuskan da dangin ubanka suke min akanka, i ave heard enough, ka tsaida matar auren kawai kowa ma ya huta, dis is ur last chance with me inba haka ba saidai kaji ayyururi, dan duk wacce nakara jin labarin cewa kana kulawa awaje ita xamu aura maka koba ka sonta wallh!.

Tsaye ta mike tana huci
"Dake nice bare agidan nan aidolene ku hade min kai kuna nunamin warayya,kowani sharri sai ace ni,kwanan nan dangin ubanka xasu ce min hala ni na haɗiye destiny dinka na aure, "komi nice, amma kai da kake ɗana nake alfahari dakai duk duniya baka ganin kunci na bare kuma xubar hawaye na.

Hawaye ta farayi cikin sheshhkar kuka tace "toh shikenan, kaje Ahmed gaka ga dangin uban naka da suke nuna cewa sune kadai suka san xafin ka,sune masu sonka kuma sune da iko

dakai,nikuma da ban da iko dakai ai Allah ne gata na. Tana fadin hakan ta fashe da kuka tare da barin wajen a gaggauce.

Jiki a mugun sanyaye ya sauke kofin shayin dayake kurba kasa bakinsa abude yana kallon yadda tahaura sama a fusace ta barshi wajen da alaman bacin rai sosai  ayayanin ta, ajiyar xcy mai tsananin nauyi ne ta kufce masa jin xuciyarsa na halbawa da wani irin tokararren damuwa, sai can snn ya girgixa kansa cikin sunkuyar dakansa kasa jin xuciyarsa na bugawa da bala'in sauri...aransa yace "this is really getting serious"...

Abincin dake gabansa ya kalla atake sai yaji komi ya sane masa, yafi minti talatin a xaune batare da yasan abun yi ba, tunani kala kala yaxo mind dinsa amma bai fahimce inda ya dosa ba, he just cant afford to make his mum cry bcos of all this dolene kawai ya nemi mafita saidai bayajin har abada xai iya kasancewa mijin kafayat. Shikan sa baisan dalilin sa najin hakan ba, haka kawai yaji aransa cewa baxai auri kafayat ba, and thinking about oda girls just make him sick sabida sunyi yawa,Adiahar can kuma tayi masa nisa,kai bama wai dan nisan kawai ba, tuna cewa sai yaje garin su ya lallabeta ya bata hakuri akan abunda yy mata yasaka yakejin muguwar kasalar karfafa magananta aransa duk dama dai itace gwamma gwamma.

But He is just not feeling intrested in begging or petting anygirl at all, duk ya rasa ta ina ne xai fara warware wann tulin matsalar tasa ,yasan dai baxai iya yanke wani hukunci aynxu ba.

Wayarsa yasaka hannu ya dauka ahankli ya bude call log ya fara scrolling Tunani kala kala yana yawo acikin kwakwalrsa.

Adede kan wata lamba da aka rubuta BANJI ya dakata, Da har xai dialling sai ya tuna yanayin abokin nasa dake son kasancewa da budurwansa hidaya a kusan kullum, karamin tsaki yaja sann ya shiga wajen text message ya rubuta sako "i need to talk to u banj! snn yatura masa baiyi ko minti biyu da turawa ba yaga reply an rubuta" is not safe,pls lets chat!.

Kai tsaye yafahimce cewa ba shikadai bane awajen dayake, dan haka babu bata lokaci ya hau rubuta masa damuwar san ta text msg din dake Banji din abokinsa ne na tun primary har sukakai secndry iya university ne kawai basuyi tare ba amma yana daya daga cikin aminansa na kud da kud.

Banji na xaune tare da babe dinsa hidaya yaga shigowar Sakon wanda ya shigo da wasu irin rikitattun bayanai na cewa Ahmed yana son yyi aure by all means xuwa next week but almost duka yan matan dake available bayason ya auresu.

Daga xaune abokin nasa yake amma saida ya mike xumbur yanamai duban text din da tunanin ko Ahmed ya samu tabun hankli ne for being dis confused, kallonsa budurwansa take har ta karaso gefensa ta tsaya ayayin da taga ya nitsu yana karanta sakon, ya memeta yakai sau biyu ita kuwa tsaki taja ta dauke kai dan ta tsani Ahmed din sosai sabida yadda yake bala'in rainawa mata hankli,bai kulata ba ya amsa shi..

Ya rubuta masa "Guy are u insane?..waime kake cewa ne.

Bai amsa shi ba ya rubuta.."Can we see now?Banj..i need to see u now..im desperate! Mamy is upset with me akan maganan auren nan.

Banji na daga ido yaga budurwansa ta tsume ta hada gabar da yamma tana watsa mai wasu uban harara masu xafi  girarsa na sama a dage ganin tayi masa alaman kar yace masa yaxo da alaman dai bata son xuwan nasa,hakan yasa yy shruging shouldern sa dan shikansa ya tsani draman su subiyun dan kullum acikin fada da juna suke. Bai turamai text ba sai kawai ya kirashi awaya, bayan kmr ringing biyu sai ya dauka suka fara magana sama sama dake budurwan tasa bata basu waje akan Ikci ba har saida taji yace masa karyaxo gidan sabida yana tare da ita.

Duk da takaicin da banji ya bashi dayace masa hakan Baidamu ba sabida a matse yake yana neman koxai samu wani mafita na daban.  A wayar kawai suka soma yin maganan since its urgent.

Bayan kasancewarsu su biyunsu awajen nan Ahmed yafara gaya masa Abubuwanda ya faru da abunda yake ji aransa.

Bayan saurararsa na dan Ikc wani Ajiyar xciya banjin ya sauke snn yace "guy calm down, indai na fahimce ka da kyau kana nufin sabida fushin mamy kake son kayi auren nan cikin gaggawa amma bawai dan kana son yi ba.. and then baka son ka aure best girl friend dinki kafayat buraimo not bcos batayi maka ba, but sabida dan kaidai baka son ita ta kasance matarka...snn sauran yan matan ma basu maka ba,and yet innocent babe dinka na can calabar itace gara gara amma baka son kaje ka bata hakuri right?..

Yace yeah..sumting like dat..

Girgixa kai banji yayy baice komi ba. Sai can snn yace okay..Ahmed, ka riga kasan cewa kai namiji ne wanda bakasan ina ka dosa akan mata ba,i mean guy, ure soo scruternixed wallhi baka da alqibla acikin burinka na aure..ure just lost.

Fusknsa a daure yace "yes am lost! thank u if dats a compliment. Since i am lost can you pls find me?see Guy Just tell me wat to do dan Allah. Wnn matsalar yafara samun damuwa. Wai ahaka bacin ran mamy fa kenan? Ran da na hadu dana baba na kam hala sai dai insha duka dan naji ance nema yake agidan kamar kudi.

Banji yana dariya Yace hmm aikai din ne bamai iyar maka sai Allah, jokes aside Lets think outside the box dan Ta hakane kawai xamu iya samun spec dinka tunda dukan wanda suke available din basune agabanka ba amma dai kasan in de kana son burinka dana mamy ya cika acikin gaggawa dole ne kayi hakuri da result dinko?

Nodding kansa kawai yy amma Baice komi ba.

Banji Yace okay i have an idea, Ahmed baice komi ba alaman yana sauraron shi,..dan shiru yy kafin nan yace "Ahmed,nace why not munemi wata babe na daban sai ayi arranging contract marriage tsakanin ku. After some months or years or so, saika saketa ta tafi basai wani abu ya shiga tsakaninku na aure ba,the marriage shud just be on paper like a name sabida kwanciyar hanklin famlynka,i am sure by then kafin contract din ya kare harka samu wata wacce kake asalin so din right?.

A mamakance sosai Ahmed yace " _kini? mi, adehun igbeyawo?_
(What? Me,contract marriage?)

Tun Kafin banji ya amsa a firgice cikin axalxala masa masifa da ihu yace "kamin shiru malam, _Ṣe o ya were? .. kini imọran aṣiwere ni banji yii?_ (kana hauka ne?..what stupid idea is this)

Murya kasa kasa banji yace. _Aaa kini, shebi dats kini o fẹ?_ (Aaa, Ba abunda kake so bakenan?) Yafada dramatically sounding irin shebi dats wat u want right?.

Ido a lumshe Ahmed yace but dats nonsense now...contract marriesh Ahhhh banjiiii _ure Egba asiwere mi ore_ (ure absolutely mad my friend)

daga kafadu sama Banji yy snn yace okay oo nide na gaya maka nawa iya naxarin,dan nasan hakan ne xaifi maka sauki nide aganina..Cos now idan ma aka samu matar auren bafa sonta kakeyi ba,Ba xaka kulata ba,toh ba gara kayi na contrct wanda xaka san yarjejeniya bane a tsakaninku tana rayuwarta kana naka?

"Yen yen yen yen malam kamin shiru kawai. Is marriage a joke to u?

Dariyar mamaki ne ya kufce wa banji Cikin dariyar yace hmmm says by the person who want to get married in two weeks amma baida tsayayyen budurwan ayanxu.

Tsaki mai tsayi Ahmed yaja cikin mita da bambami mai yawa kamar matar mamaci yanacewa _i'm daju dat gun ọfun ọrẹbinrin ti urs ti mu u_( I am sure dat long throat girlfriend of urs has intoxicated u)..

Banji yace ahhhhhhhhh damilare Ahmed bello pls do not insult my swt girlfriend, errn aigara ni na ajiyeta kuma ina sonta snn auranta xanyi..

Cikin katsesa Ahmed yace shut up ure in lust jare, fuck u both. But Its okay sha ka aje wayarka kusa xan kiraka anjima idan nagama tunani And dont expect me to thank u for this stupid advice oo. _O ya were,look at u, Awon contract marriesh gang,mtsssss_ Har ya katse wayar banji bai dena dariyarsa ba.

Bayan nan ya dade a xaune akan chair na dinning table din yana juya maganan banji acikin

ransa,saidai ta duk inda ya bi da maganan sai yaji hakan bai masa ba, duk ya rasa meke masa dadi, yasan kuma idan ya nemi wani extra shawara daga wajen dayan abokinsu bankole abu dayane kawai xai gaya masa cos he is a party boy,yasan cemasa xaiyi ya shirya suje club yy wa wata cikin shege su haifi dan sukawo gida cos aganinsa a grand child is wat our parents want,and he cant do that ko dan for the sake of his mamy, dan duk iskancin shi dai bai taba aikata xina ba sabida iyayensa sun bashi ilimin addini sosai, mikewa yy jikinshi duk babu kwari snn ya fice daga sashen yana tafiya ahankli yana kallon agogon hannunsa, gun motarsa kirar Lexus ya nufa cikin kankanin lkcin ya bar cikin gidan nasu.

tafiya yake ahankli akan titi har ya iso wani layi da ake saida manja,equshi, da busashen kifi wanda mafi akasarin mutanen wajen  inyamurai ne,rage tukin yy sabida cunkuson jama'a, ya shiga murxa stiring motarsa ahankli yana dan satan kallon wata poster da akasa abakin wani shago na ogoja market Festival in calabar. Lokaci guda mind dinsa ta daka tsalle kwakwalarsa ta hau tuno masa wann ranar being the first day daya soma cin karo da kyakkwan fuskar yarinyar nan ADIAHA agarin calabar.

Hanyar dake 61,Aguiyi ironsi street yabi ixuwa maitama district hospital inda yake da first casual appointment dinsa nayau  ahankli yake tuki danhar ya isa bakin gate din asibitin tunanin abunda ya faru a wann ranar festival din yakeyi aransa Da kwakwalrsa..

After some few minutes ya kammala aje motar sa acikin parking space na hospital din, sauke ajiyar xuciya yy kafin nan ya sauko dauke da jakar laptop dinsa yana tafiyar sa mai aji kowani step dinsa acikin nitsuwa wanda ko kallo daya kamasa baxakace yana cikin wani damuwa ba.

Direct ya haura sama private office dinsa dan shi babban consultant ne a asibitin yakan duba files din duk wani cases na marasa lpya daya shafi communicable diseases.

After 20 minutes.

Zaune yake akan kujeran haɗaɗɗen office ɗinsa wanda yake juyawa dashi ahankli ga wani sanyin a.c mai qauraye da qamshin turaren sa daake tashi ahankli yanamaai mamaye wajen, sosai office din nasa ya hadu, yana ɗauke da set ɗin 2 L shape cushions, table da kujerun xama na patient, sai gadon dubiya, fridge da doctors Cabinet.

Daga gefensa kuma show glass shelf ne wanda yake shirye da Awards da frames ɗin hotuna insa da yake sanye da convocation gown as the best overall medical student in uni of ibadan,obafemi awolowo uni, ɗayan frame ɗin kuma duk honors dinsa na U.K da manchester ne he is also the best, sai ɗayan kuma da Labcoat da electronic microscope ayayin dayake gudanar da disease research a calabar national science laboratory..

Kallon hoton ya dinga yi yana tunowa da fuskar Adiaha tana masa murmushi..dafe kansa yy aransa yace ohh Allah!! Ni kode yarinyar nan ta mutu ne..haka kawai seta fadowa mutane arai?

Knocking ƙofar aka yi wanda ya sashi katse tunaninsa,nurse ce ta nemi ixini kanta a sunkuye a ƙasa, hade rai yy bai amsa ba ya bude wani file ya fara rubutu sai can kmr after 3 mins snm ya bata izinin shigowa ciki,Da sallama a bakinta ta shigo ta gaishe sa bai amsa ba yace "what?..bakinta na dan rawa ss..sir..you have a call from..tun bata karashe ba ya datse ta cikin ixxa yace "where?
Speak fast..kina wani abu kamar doluwa..

Da kyar ta hadiyi yawu cikin gaggawa snn tace "Dr hassan's hospital sir..its an emergency... They..

Ya kara datse ta
"....Need my urgent attention?

Tace "ohhh, yes sir!..

Daga nan bai kara kulata ba ya cigaba da abunda ke gabansa harta gaji da tsayuwarta ta bar wajen.

Fitar ta keda wuya ya dau wayarsa ya wuce Dr hassan's private hospital dake iller cresent, no 5 katsina ala street cos is not far, duk dai acikin maitama din yake.

Yana isa ya ci karo da dayan abokin nasu Doctor ibrahim bankole suna cemai Banky anan shi yake aiki he is a correct sugeorn shiyasa idonsa idon mata lolz.

